Ɓangaren Su Ammie kuwa Umma da Hajiya Balki da sauran matan gidan banda godiya babu abun da suke yi , Haka Baba ya shigo yayi nasa . Umma ta so ta ƙwana ganin yamma yayi amma Ammie tace a yau zasu koma. Sallama sukayi bayan sallar magriba Umma har zaure, su Baba Sule kuwa har bakin moto da su aka je. Umair ne ya jira fitowar Umaima don suyi sallama. Wannan yasa shi bai bi zugar Ammie ba. Ba don taso ba Umma tace tazo suyi sallama ,

saboda bata son Umma ta fahimci Wani Abun ne yasa ta fitowa kaman yanda tace . Koda ta iso zauren shiru tayi tana jirar jin mai kuma zaice. Kusan mintuna biyar sannan ya motsa bakin sa yana cewa " Ki sanar da Baba Nan da 2weeks Daddy zai zo maganan Auren mu , saboda a wannan satin za wuce Oustralia.

Kallon sa tayi kamin ta sa wani irin dariya na rainin Hankali. Amma lallai Umair ka iya rainin hankali, Waye za'a yi maganan Auren nasa Ni?? Allah yayi mun tsari na haɗa zuri'a da mazinaci.! Mugu.!! Mun rabu nida kai rabuwa ta har Abada. Baiyi mamakin furucin ta ba duk da bai taɓa tunanin zata ƙwantar masa da kai don tace masa a'a ba. Murmushi yayi yana dannewa wani ɗaɗɗatan abu da ya tokare masa a maƙoshi. A hankali ya tako kusa da ita.

Hannun sa yakai yana riƙo nata tare da yi kaman zai shige mata. Saurin ja baya tayi ganin yanda yake shirin mata iskancin da ya saba. Nan fa zauren gidan mu ne yanzu zanyi maka ihun ƙwarto .! Ƙara sakar mata murmushi yayi. Lallai wannan Ɗan duniya ne . Tayi maganan a zuciyarta . Tsinkayar Muryar sa taji yana cewa " Dama ai bance da Amincewar ki zan Aure ki ba ,amma ki sani sai na Aure ki ,ko kina So ko Bakya so.! Ina da wanda zan Aura , ba kai ba ,ka jira zaka ji labari Inshaallh. Baya yayi yana dariya kana yace " Ohk kina Son shi kenan wanda zaki Auran? Ohk a shawarce ki Aure Ni ,Don bazan bari kije mawa wani a matsayin ragowa ba. Wani irin ɓaci ranta yayi nan da nan kawai sai ga Hawaye shar shar . Sai na dawo.! Yayi maganan yana juyawa tare da barin ta nan tsaye.!

*MMN TEDDY*
*M*

*Littafin THE SEXY BOSS na kuɗi ne ban yarda ki karanta mun ba tare da kin biyani haƙƙi na ba... Regular group ₦300...Vip group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko kuma ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932 Idan VTU transfer zakiyi ki tura kai tsaye ta wannan number 09061466409*

RAMCY HERBAL💃💃Tabbas da kaji wane ba Banza ba , wani kaya sai amali , rugun babban motsi , margamargan dutse kafi gaban Aljihu ,wannan nima kaina da baki na na faɗi haka yake🤞. Ina kuke ƴan Uwana manyan mata ,shin kuna ina?💃 Matso kusa ga babban dama ta samu daga hannun wannan shahararriyar ƴar mutan Sokoto RAMCY HERBAL ta shirya tsaf don kawo mana magunguna da dama meye matsalar ki Amaryar Oga??
Uwar gidan Alhaji kefa? Maza saurara kiji wannan magunguna daban ne da saura daga taskar ƴar mutan Sokoto .
-Maganin ƙanƙancewar gaban ɗa namiji
-Maganin sanyi na mata da na maza
-Gumbar riɗi , gumbar aya ,gumbar ƙwaƙwa , gumbar dabino.
-Zumar ni'ima

-Zumar ƙiba
-Zumar goran tula
-Dambun ni'ima
-Zumar ƙwakwa da ta dabino
-powder hip up Dana breast elargement .
-tsumin ƴar gata
-Tsumin tabaje
-Maganin ciwon sugar
-Maganin hawan jini
RAMCY HERBAL ba anan ta tsaya ba ,  ta kuma taho mana da kayan gyarar jikin mu...💃💃
-Dilka Soap
-Whitening Cleanser
-malato soap
-Half cast soap
-shu'umin Humra tare da turaruka masu ƙamshi ,da zai rikita Oga in a few sec.
Ga masu buƙatar ƙarin bayani maza hanzarta ku tuntuɓi wannan number 07032209881 / 08109511467 .
Address: Sabon titin sokoto rima , kafin wajen sha'aban mai kankana mun gode.!

Tsayawa Umaima tayi nan Wurin motsi ta kasa sai aikin sharar ƙwallah tana tunanin Maganganun Da Umair ya gama watsa mata . Hango Baba Sule Tayi daga wajen soron yana takowa da'alama shigowa zauren gidan zaiyi ,nan ta yi saurin juyawa tana nufar cikin gidan. A tsakar gida ta tadda kaf matan gidan , da sauran mutane wanda su taho mawa Umma jejeto ,wuce su tayi ba tare da ta tanka kowa ba , Tayi cikin ɗakin Umma .

Tun daga Wannan rana Hajiya Balki ta yanke hukuncin kar a bar Umaima ta fita ko nan da can ,Bata ba fitar gida,kullum tana zaune gu ɗaya. Fatima ce da sauran ƙawayen ta ke shigowa suna tayata fira.  Idan Umaima taji har hantsi yayi Fatima bata zo ba ,zata aika a kirata su zauna fira.

Zaune Umaima da Fatima suke , Suna cin Tuwon da Umma tayi shi yanzu da wannan yammacin . Umaima wai naji baki mun maganan Kuɗin bane ? Wannan matan data kawo ki itace ministan ko. Ke amma fatima baki da hankali wallahi , wannan mutfa fa da kika munzo tare dashi ai shine Umair ɗin ,ita kuma watan nan matan mahaifiyar sa ce. Nan Umaima ta cigaba da laburta mata abubuwan da suka faru , don har Lalatan da yayi da ita bata ɓoye mata ba . A ƙarshe ne ta faɗa mata maganganun da yaɓa mata a zuwan nan da sukayi tare . Tun da Umaima ta fara bata labarin Yanda suka yi da Umair Fatima ta fara zubda Hawaye . Kai Amma wannan Mutumin mugu ne Wallahi babu na biyun shi. Hala ma shiyasa kika amince da Ashiru don nayi mamaki da kika yarda ki Aure san.   Eh fa ,don dana Aure Umair gwara na Auri Ashiru ko banza nasan shi ba mazinaci ba ne. Kuma ki sani wallahi ba sona tsakani da Allah Umair keyi ba ,kawai don nayi masa mugun baki ne .

***

Ɓangaren iyayen Ashiru kuwa ,tun da suka zo kaico kaico Suka yi magana da Su baba Sule akan tsaida Auren Umaima da Ashiru. Wanda hakan yasa su Amincewa tare da Hamdala . Sati uku aka sanya na Auren , don an fi tsawon shekara guda dama ana Son tsaida magana Umaima ke kauce kauce tayi ta masifa ita bazata Auri Ashiru ba ,sai ta gama sakandire. Sai a yau su Baba suka tsaida rana .

Kowa a dangi farin ciki yake yi da Wannan Aure , duk da Umma bata aje ba,ba kuma ta bai mawa wani Ajiya ba . Amma tace Allah shi ke rufa asiri .

Wasa wasa lokaci nata tafiya , yau gashi saura ƙwana shida bikin Umaima da Ashiru , a wa'ancen ranakun sam ko tuna Umair bata yi , amma sai a yanzu tayi ta tunanin sa , sosai take tambayar zuciyar ta mai yasa take hakan ,don so take ta manta shi a rayuwar ta , wanda a cikin zuciyar ta ta yi masa suna da "Mayaudari. Fatima ne da ƙawayen Umaima suka shigo gidan , a bakin Kitchen suka tadda Umaima tana rafka tagumi kaman yanda ta saba da kullum. Cikin sauri Fatima ta ƙarako inda Umaima take tana cewa ":Ga Ashiru can a waje yana jirar fitowar ki ,shida Abokin shi . Tashi muje nasan bai wuce hidimar bikin ne .

Nisawa Umaima tayi tare da ɗaga kanta sama , ganin hijabin ta a saman igiyar shanya yasata raruma tana sanyawa tare da cewa " Ku mu je ko.! Tun daga nesa Hango Umaima Ashiru ke washe baki , har suka iso . Gaishe su Tayi cikin mutuntawa , don Umaima ta sauya ƙwarai kaman ba ita ba . Kullum a cikin kasale da zazzaɓi take wanda har Muryar ta ya sauya , yawan hargogowan nan duk ta daina shi . Malama Umaima ya hidimomin? Da kuma shirye shiryen? Cewan Ashiru yana murmushi . A hankali Umaima tace " Lafiya lau ya naku shirye shiryen ?. Alhmdllh cewan Ashiru yana faɗaɗa murmushin sa . Yanzu da Aƙwai wani Abu da kuke buƙata ne?.

Juyawa Umaima tayi tana kallon Su Fatima da suka amshe ta suna cewa " Sai dai za'a bamu kuɗin walimar ƙawaye. Hummmm Ni Bara na shiga daga ciki idan kun kammala ku sameni a gida . Umaima tayi maganan tana masu Ashiru sallama tare da juyawa tana nufar cikin guda .

Can ƙuryar Ɗaki ta shige tana ƙwanciya a gadon Umma tare da rufe idanun ta kaman mai jin barci . Motsin Shigowa taji wannan yasata buɗe idanun ta tana kallon Umma dake shigowa. Miƙewa tayi zaune , Nan Umma ta zauna bakin gadon tana kallon Umaima kaman mai tsartan Wani Abu ,sai kuma tanisa tare da cewa " Umaima kina lafiya kuwa? Meke damunki kwana biyu ?. Nisawa Umaima tayi kana tace " lafiyana qlau Umma ,kwana biyu zazzaɓi ne kawai sai yawon kasala da nake ji. Bari Malam ya shigo sai a aika chemist a sayo maki maganin zazzaɓi . To Umaima tace tare da lumshe idanun ta. Miƙewa Umma tayi tana fichewa daga kuryar dakin , a zuciyar ta tana tunanin ƙila zullumin Aure ne ke saka Umaima hakan.

***

Ɓangaren Umair kuwa a sati biyu ne yaso ya dawo gida nageria , kullum tunanin sa yana kan Umaima , Aikin nasa ne yaga zai ɗauke sa fiye da sati uku ,wannan yasa shi a sati na Ukun ya kira yayan Mahaifin sa yana sanar masa da Batun Umaima tare da roƙon sa kan a je a nema masa Auren ta . Cike da jin daɗi Alh Iblo yake sa masa Albarka ,don dama burin su suga Auren Umair ɗin . Yana datse kirar Ya kira Alh. Ahmad moddibo yana sanar masa kan zai je nema mawa Umair Auren Umaima anan Garin su. Sam Daddy Bai jah ba ,hasali ma addu'a yayi na nasara.... Ana saura kwana uku bikin Umaima Alh Iblo ya taho nema masa Umair Auren Umaima . Wanda Anan ne yake jin an kusa bikin ta saura kwana uku ma yanzu haka . Shiru Alh Iblo yayi kamin yayi masu fatan Allah ya basu zama lafiya. Godiya Su Baba Sule Sukayi ta masu tare da masu haƙuri . A haka Alh Iblo ya tafi . Bayan tafiyar Alh Iblo ne Ya kira Umair a waya yana bada baki da basa haƙuri ,sannan ya sanar masa da Cewan An mawa Umaima baiko da wani ,yanzu haka ma saura kwana uku bikin . Ai bai bari ya ƙara ji daga bakin da ba , ya katse wayar yana sawa a yankan masa tikitin tafiya , don a cewan shi a washe gari zai dawo gida Nigeria , sam ba zai bari ayi wannan Auren ba .!

Kuyi manage wannan Pls ba yawa 🙏
*N*

*Littafin THE SEXY BOSS na kuɗi ne ban yarda ki karanta mun ba tare da kin biyani haƙƙi na ba... Regular group ₦300...Vip group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko kuma ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932 Idan VTU transfer zakiyi ki tura kai tsaye ta wannan number 09061466409*

*Night Update🥱*

Hankalin Umair sosai ya tashi da jin maganan Alh Iblo , wanda bai shawara da kowa ba ya yanke hukuncin dawowa Gida Nigeria . A kusa can Abuja Daddy ne ke sanar mawa Ammie abun da iyayen Umaima suka faɗa mawa Alh Iblo na An riga an mata miji sai dai Umair yayi haƙuri . Shiru Ammie tayi tana faɗawa Duniyar tunanin ya Umair zai amshi wannan zance? Anya zai iya haƙuri kuwa? Don a ƙwayar idon Umair take ganin mahaukacin Soyayyar Umaima , wannan yasa yana ɗaya daga dalilin da ta amince da maganan nasa bata ɗauke shi a shirme ba. Sauke Ajiyar zuciya Ammie tayi tana kallon Daddy kana tace " To Allah yayi mana zabi mafi alheri . Amin ya Allah Daddy yace , kana Ammie ta muskuta tana fitowa daga Part ɗin Daddy , Direct Bedroom ɗin ta ta nufa . Bedside Drower ta Kai hannun ta ,tare da ɗaukar Wayar ta ,don

ta kira Umair ta rarrashe shi ,ta kuma basa haƙurin matar mutum bata taɓa Auren mijin da bana ta ba . Abu kaman Wasa ta kira layin sa yafi sau biyar amma switch up .wannan yakuma ɗaga Hankalin Ammie ƙwarai . A wannan ranan dai barcin ta rabi da rabi ne.

Ɓangaren Umair kuwa ƙwana yayi zaune yana jin wani irin zafi a zuciyar sa , a cewan sa shi sam bai taba niman abu ya rasa ba . Bai kuma taɓa ƙwalla fa rai a abu bai samu ba. A kan ta baza'a fara ba. Ƙwana yayi yana shan sigari baya duba koda lafiyar sa . Cikin matsanancin ɓacin Rai yake furta " duk wanda yayi kuskuren Auren matar shi sai yasa shi ya ƙare Rayuwar sa A gidan Kaso na har ƙarshen rayuwar sa. A washe gari ne Umair ya taso daga jirgin Oustralia zuwa gida Nigeria .

***

Wani irin dariya Hajiya Turai tasa kamin ta juya tana kallon Aminiyar tugun ta wato Hajiya mulaika . Masha'allah Allah mun gode maka , da wannan Aure ba'a bashi ba , don tamkar shigar sauri yayi mana ,ya kauce mawa tugun mu. Don haka yanzu wasan zai fara . Kyacewa da dariya Hajiya mulaika tayi tana miƙamawa Hajiya Turai hannu suka tafa . Ƙwarai Turai wannan gaskiya ne , kinga sai mu zabo masa ko wacece muce zamu yi masa Auren Huce takaici. Eh kuma da Hjy mulaika kin kawo mafita kwarai , to mai zai hana Musa Ru'aifa?. Wani irin Kallon Hajiya mulaika take mawa Hajiya Turai kana tace " A'a wanda zaki saka ,sai kin tabbatar jikin ki ne , saboda kin san fa komai ba don Allah zamuyi shi ba. Na farko asirin sa zamu tona a duniya ,ko ta hanyar sharri ne ,dole gwamnati ta ɗauki mataki . Daganan ne zamu fara cin dukiyar sa ,muyi facaka da ita . Shiru Hajiya Turai tayi sai kuma tace " To yanzu wazan hada shi da ita ta kuma iya mun wannan Aiki ,cikin sirri?.  Gyara zama Hjy mulaika tayi kana tace " Baga ƴata Nusaiba ba.! Sauke numfashi Turai tayi cike da farin ciki tace " Ƙwarai kuwa ,yanzu idan kin koma sai ki mata bayani , Ni kuma zan samu mahaifin sa da maganan ,nasan dole zasu amince ,tun da babu wata mafita bayan hakan.!

****

A hankali suke tafiya kusan su Biyar hannun su duka kowa yasha lallin fulawa mai ƙyau ciki harda Amarya Umaima ,  wanda a yau biki saura Ƙwana biyu. Yaran layin kunsan Amarya da farin jini haka kowa kebin ta irrrrrr.

A zaure ne sudai su Fatima sun ga Umaima ta saki wayar hannun ta yayi ƙasa tana furta ' Innalilahi wa'inna ilaihir rajiun . Kallon kallo suka tsaya suna yi ita da Umair .wanda ganin ta yasa duk wannan raɗadin da yake ji ya ƙwaranye. Umaima Yaudara ta zakiyi? Wani zaki Aura bani ba? Anya kina Son shi kuwa? Hummmm Bakya son Umaima da kina Son shi ba zaki taɓa fitar dashi a matsayin mata miji ba ,bayan kin san nine Mijin ki.! Zaki jefa rayuwar sa cikin haɗari maslaha ɗaya ki hakura da wannan Auren idan ba haka ba ,kin fi kowa sanin ko Ni waye .! Na baki Daga yau zuwa gobe Duk shawarar da kika yanke , ga card ɗina ki Kirani. Ya ƙare magana yana wurga mata card tare da ficewa . Nisawa Ummalo tayi ƙawar Umaima kana tace " Wannan

me baƙar tabarau ɗin Waye kuma ? Umaima kin san shi ne.??. Shiru UMAIMA tayi tabbas maganan Umair ya firgita ta ƙwarai . Duƙawa tayi a hankali tana share hawayen fuskar ta ,tare da sa hannun ta tana ɗaukar katin....!

*MMN TEDDY*
*O*

*Littafin THE SEXY BOSS na kuɗi ne ban yarda ki karanta mun ba tare da kin biyani haƙƙi na ba... Regular group ₦300...Vip group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko kuma ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932 Idan VTU transfer zakiyi ki tura kai tsaye ta wannan number 09061466409*

*Morning update🥳*

Miƙewa Umaima tayi jiki a sanyaye tana kallon Su Ummalo da Fatima , kana tace "kumu tafi !. Bin bayan ta suka yi yayin da Fatima ke faɗin mun shiga uku.!! Ɗakin Hajiya Balki suka shiga don tun da bikin ya ƙara so kusa ta tattaro ta dawo gidan da zama ,a cewan ta ba zata koma ba sai anyi biki an watse . Tun da suka shiga ɗakin Ƙawaye da Son jin gulma sukayi ta baza idanu wai ko zasuji Umaima tayi magana Umair , amma kuma shiru , a haka da ɗaya da biyu kowa ya watse ,don Umaima katin Hajiya ta ɗare tana juya masu baya kamar mai barci ,amma nan kuwa sam ba haka bane , damuwa ne ya taru ya lulluɓeta . Rintse ido tayi tana saurun buɗe su ,hango fuskar Umair tayi tana sakar mata wannan murmushin nasa , hushiryar sa da ya raba tsakanin fararen haƙoran sa na bayyana. Ɗan tsaki ta jah kana ta furta mugu kawai . Jin wannan magana nata yasa Fatima da ita kaɗai tayi saura cewa " Umaima wai ya ake ciki ne? . Juyowa Umaima tayi tana muskutowa daga ƙwance bata tare da ta miƙe ba tace " Kaman ya kenan Fati.." hummmm sauke numfashi Fatima tayi kana tace" Umair ,Ni anawa ganin mai zai hana ki Auri Umair kaman zai fi mana , kiyi duba fa , da gaske yake a yanzu . Wani irin murmushi Umaima ta saki ,kana tace " Baki san waye shi bane,Amma ina da yaƙinin Umair ya Aure Ni to ba zaman daɗi zamuyi ba ,mugu ne macijin sari ka noƙe ,azabtar dani kawai zaiyi ,don duk izayar nN da yayi mun bai ishesa bane shiyasa yake son Aure na ta rabani da duk wani farin ciki na. Kar fa ki manta da baki nayi masa kan Allah yasa ayi mawa ya'yan sa haka shine yace " Zai Aure Ni don dole.

Shiru Fatima tayi kamin kaman wanda aka tsikara tace " Amma dai kin san kunfi dacewa dashi ba Ashiru ba. Dacewa.? Umaima ta maimaita maganan kamin ta taɓa baki tana faɗin , idan na Aure sa da wannan ƙanƙantan shekarun nawa ,kashe mun Rayuwa zaiyi ,matar shi kan ta abun ki tausaya mata ne ,mugu kawai ". Umaima tayi maganan tana tuno da maganan sa da yake cewa " Ni bana barci da kaya , haka kuma nake son Matar da zan Aura ta kasance. Hummmm

to ai shikenan Umaima kin fini sanin waye shi ,tun da ke kika zauna dashi . Cewan Fatima tana murmushi .

***

Bayan Umair ya fita ne yana shirin fita layin ya haɗu da Baba Sule , Wanda kallo ɗaya yayi mawa Umair ya gane sa . Cikin matsanancin Fara'a ya kalli Umair da shima shi yake kallo " Cikin mutuntawa Umair ya gaishe da Baba Sule ,kana Baba Sule ya amsa yana faɗin Saukar yaushe ? Ko kun zo ɗaurin Auren ne?. Wani irin bugawa ƙirjin Umair yayi sai ya ɗan yi murmushin yaƙe yana cewa " Ina Baba.? Au Baku haɗu ba kenan da Malam Ibrahim ?.  Eh Bamu haɗu ba. To muje Na kaika shagon shi. Shiru Umair yayi yana bin bayan Baba Sule , a zuciyar shi yana cewa " Dama Baba Kasuwanci yake yi?. Gani yayi sun fito bakin hanya Baba Sule na shirin tare Abun hawa .! Cikin sauri Umair ya ce dashi" Ah Baba baga mota na can mun barota ta a layi, mai zai hana muje mu shiga sai muje Ai ban kawo shagon da nisa ba. Murmushn su ta manya Baba Sule Tayi kana yace " Ai shagon a kasuwa take . Juyawa sukayi tare da nufar Moton da Umair yazo da shi kirar wane yaro . Suna shiga Umair ya fara driving basu ɗau mintuna goma ba suka isa kasuwa . Bin shagon Umair yayi da kallo ,shago ne ɗan madaidaici , ga yaran shagon suna ta sallamar customers . Ɗaga kansa sama Umair yayi yana duban Shagon ,anan ya fahimta shagon siminti ake sayarwa . Ba Bismillah Umairu shigo daga ciki ,cewan Baba Sule yana shiga Umair ya biyo bayan sa.  Masu saye da sayarwa wurin duk idanun su ya dawo kan Umair , kowa na tunanin ne ya kawo wannan matashin attajirin nan cikin kwacalcalin Kasuwar ? Wai kuma ya rasa inda zai zo sai shagon sayar da siminti .

Zaune Baba yake akan Sallaya yana zikiri don rana yana gab da faɗuwa.  Shafa addu'a yayi yana kallon Baba Sule da Umair da suka zauna a gyefe suna jirar kammalawan sa .aaa Umairu kune da yammaci?. Murmushi Umair yayi yana sunkuyawa cike da ladabi yana gaida Baba ,kana ya baba ya amsa yana tambayar sa kowa da kowa. Ba tare da Umair ya basa Amsa bane ya kalli Baba Sule kana ya juya yana kallon Baba tare da cewa " Baba Wai Shin gaskiya ne an mawa Umaima miji bani ba?. Kallon sa Baba Yayi kana yayi  shiru sai kuma ya ɗago a yana girgiza kai tare da cewa "Ƙwarai Umairu , yau saura kwana biyu kenan. Sai daga baya Aka zo da maganan ka , haƙuri xakayi Allah ya baka wata wacce tafi Umaima.

Ina Baba bazan samu ba. Yayi maganan idon sa na kaɗawa daga fari zuwa ja. Umaima ba matar kowa bace ,matata ce.! Baba don Allah ku warware wannan Sa ranan A maida akaina. A jibin a bani ita . Ƙara ware ido Baba yayi cike da mmki , kamin yayi magana Baba Sule yafara ba Umair haƙuri ,tare da masa bayanin idan suka raba wannan Aure sunyi ƙaranta ,kuma sannan Mutan unguwa zasu ce sunyi Auren kudi ne , kuma kar ka manta Umaima ba tsarar Auren ka bace ,ka fita komai . Cewan Baba yana kallon Umair wanda jijiyoyi n jikin sa sun tashi , gargasar hannayen sa sun mimmiƙe . A hankali ya furta " Shikenan Baba Allah ya basu zama lafiya." Amin su Baba suka amsa .

***

Tun daga wannan Rana Umair barci ya gagare idon sa. Yayin da zuciyar sa ke saƙa masa abubuwa da yawa da zaiyi akan Umaima ,don har tunanin yasa a sato Masa ita sai da yayi , ya kulleta a tare dashi suyi rayuwa har mutuwa . Amma tuno da karamcin wannan gida yasa shi fasa yin hakan . Kullum a tunani yake a kuma shan barasa . Zaune yake shida Julayb ,Julayb ne ya aje karan sigarin kana yace "Wai Umair kana da hankali kuwa? Akan mace kake kokarin kashe kan ka ?. Jubi fa kwalebe nawa ka shanye na barasa baka tunanin lafiyar ka?. Banza Umair yayi masa kana cikin Muryar maye yace " Kaje Garin su Umaima yau ka gani an ɗaura mata Auren?. Kallon sa Julyab yayi kana yace " Idan an ɗaura to me xakayi? . Cireta a rayuwa ta zanyi. Murmushi Julayb yayi ba tare da ya bari Umair ya fahimta ba yace " To yau zan tafi ,tun da kasan yau ne ɗaurin Auren ..

***

A yau asabar ƙarfe biyu aka ɗaura Auren Umaima da Angon ta Ashiru . Wanda tun da Aka ɗaura Auren nan Ashiru fara'a bakin sa yaƙi rufuwa ,haka mutane da dama sun halarta wannan daurin Aure ,don Baba aƙwai shi da mutane kwarai.

Tun da aka ce an ɗaura Auren , Umaima hankalin ta ya fara tashi , babu tunanin wanda take yi sai maganan Umair.! Yaudara ta zakiyi???. Wani irin bugawa ƙirjin ta yayi tuno da wannan maganan tasa . A haka ta wuni babu walwala . Wanda da misalin yammaci aka kawo mota aka ɗauki amarya zuwa gidan mijin ta wato Ashiru . Don basu da nisa daga layin su Umaima sai inda aka kaita . Gidan yawa ne don a cikin gidan aka yi mata ɗan Platt Mai ƙyau. Mata ne kusan bakwai a gidan kowa da mijin ta da yayan ta . Kuma duka yayyun Ashiru ne .

Su Fati kuwa sai fara'a ake ,ana ta shiga da fita , wanda wuraren ƙarfe takwas kowa ya watse . Abun da Umaima bata taɓa gani ba shi ta gani. Bayan Mutane sun watse ne , Ashiru ya shigo da yayyun sa mata don shine karamin su , acewan su sun rako Auta ɗaki. Wani sarawa kan Umaima yayi cikin ta na murdawa sakamakon jin ƙamshin turaren Angon nata , wannan yasa ta saurin miƙewa tana sauke mayafin da aka rufa mata . Muryar babban yayan su taji tana cewa " Alhmdllh Mun kawo Angio....kamin ta rufe baki ne Umaima ta fara amai , kaman zata fidda hanjin cikin ta ...!
*P*

*Littafin THE SEXY BOSS na kuɗi ne ban yarda ki karanta mun ba tare da kin biyani haƙƙi na ba... Regular group ₦300...Vip group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko kuma ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932 Idan VTU transfer zakiyi ki tura kai tsaye ta wannan number 09061466409*

*NIGHT UPDATE🥱*

Tsayawa Duka dangin Ango Ashiru sukayi kana Yaya Hadiza tayi saurin nufo Inda Umaima ke tsugune tana sheƙa amai kaman zata fidda ƴan hanjin ta . Tallabota Yaya Hadiza tayi kana tace " Umaima lafiya dai ko. Babbar yayan su Ashiru ne cike da masifa ta kalle Umaima tana  cewa" Wani lafiya ,ai dagani kun san babu lafiya wannan. Sam Ashiru ba zai ƙwana a ɗakin nan ba , sai an tabbatar Wannan yarinyar ba ragowa bace. Subhanallah Yaya Uwauwa wannan maganan bai dace ta fito daga bakin ki ba ,da girman ki fa?. Cewan Ashiru cike da damuwa . Kai da Allah wuce ka rufe mun baki , Kai yaro ne , Kalli fuskar ta , kasan a haife na haifi Umaima don na kusa jika da ita . Ba yau nafara ganin mace watsatstsiya ba. Don haka A kiramun Safara'u maƙociyar mu yanzu ,tazo tayi gwajin fitsarin Ta ,ko anan zamu fahimta gaskiyar Al'amarin. Juyawa Umaima tayi tare da durƙushewa anan wurin. Tana sakin wani marayan Kuka kana ta fara cewa " Umair ka cuceni ,ka cuta Rayuwa , Bazan yafe maka ba ,wayyo Ni ,wayyo Rayuwa.! Juyawa Yaya Uwauwa tayi tana kallon Yaya Hadiza kana tace " Kunji magana ta yafito ko?. Hummmm a jura zuwa rafi dai . Shiru Falon yayi kowa da abun da yake saƙawa a zuciyar sa na tsawon minti ɗaya . Kana Yaya Hadiza ta cika hannun Umaima tare da jan wani dogon tsaki . Ai dama wannan shaka shaka na wannan yarinyar Ni tuni ina zargin ta . Allah shi kyauta kai ka nace gashi nan ta jawo mana Abun magana a maƙota da dangi ,a koma ana cewa ka Auri karuwa.! Yaya Hadiza ke maganan cikin matsanancin fushi tanayi tana kallon Ashiru da ya sauke hular shi yana firfita don wani irin gumi ke karyo masa .

Yaya Uwauwa ce ta amshe Hadiza da cewa " Ai wannan tafi ragowa karuwa dai ,gatanan ƴar malam taƙi halin malam ,waye bai san mahaifin ta ba , shi fa yake kirar sallahn masallacin layin nan , wallahi kin fita Zakka a cikin yan uwan ki da gidan ku baki ɗaya . Kin kuma jawo mana Abun kunya a idon duniya . Tana gama faɗin haka ta juya fuuuuu. Yaya Hadiza ce ta kalli Ashiru dake tsiyayar da ƙwallah . Umaima.! Ya kira sunan Umaima da a yanzu kukan ya gagara mata sai sauke ajiyar zuciya ,tana cura ji take kaman ta haɗiye ranta ta mutu ta huta. Tana nan zaune ne taji y Kira sunan ta , wanda sam ta kasa Amsa shi ,sai numfarfashi da take yi ,ji take ƙirjin ta na mata zafi kaman zai ɓalle wani ya fito mata ta huta . Umaima me yasa kika yi mun haka?. Ba laifi na bane , Shi ne ya mun haka?. Auwalu??? Ashiru yayi maganan cike da fusata ,don shi har a yanzu bai ɗigon raguwar soyayyar Umaima a zuciyar sa ba ,sai ma wani wutar soyayyar da yake ƙara mamaye zuciyar sa. Kaman ba zata basa amsa ba , sai kuma tace " Sir Umair Ahmad moddibo.! Wani irin bugawa zuciyar Ashiru yayi ,don tabbas yasan Umair ba ƙaramin mutum bane a Nigeria baki ɗaya ,ba state ko ina na Nigeria ambaton sunan matashin ake yi. Cikin gwasalawa da wawantar wa Yaya Hadiza tace " Au iskancin naki har ya kai ga Nan? Kin san waye Sir Umair kuwa da har zaki masa wannan sharrin , don an kawo ki gidan mijin ki a ragowar ƙattai . Kinje wani ƙato ya gama buga maki iska sai Kizo mawa ƙaninmu a matsayin ragowa . To hattara kar ki ƙara faɗin munin abu akan Sir Umair , don kaf dangin ku zai ƙarar Bakya kaɗai ba ,mubafaka muguwa kinci mana mutunci tsakanin mu dake ALLAH ya isa.!

Wani irin fashewa da kuka Umaima tayi tana ɗaura hannun ta aka ,sam ta rasa me ma zata ce fadi take wayyo Ni Umaima ,Ni naja wa kaina ..! Kai Da ALLAH sake ta yanzu ka fito ,iyayen ta da suka kawo mana Ragowa gindu a fafake su taho su dauke ta ,don har da ajiyar ƙwarto.' girgiza kai Ashiru yayi kana yace " Ina son ta a haka , ku barta zan Zauna da Umaima , har ta haifi ɗan ta ko ƴar ta zan riƙe su mu cigaba da zama har Abada...sakarcin banza ,au Dama Kai shashasha ne nasani . Idan soyayya ya rufe maka ido ,mu namu idon a bude yake ,yanzu wannan shedaniyar a yau sai ta bar gidan nan.!

***

Umair lafiya me yake damunka haka?. Ammie ke Tambayar sa cike da mamaki ,Daddy ne yake furta Umair kana lafiya kuwa? Kasan me kake sha a tsakiyar falo? A gaban ma'aikata ,idan baka ji kunyar mu ba ,ai kaji tsoron Abun da mutum zai je ya faɗa. Wannan fa giya ce.! Cewan Daddy Yana pointing ɗin Ƙwalbar barasan da hannun sa . Meye Daddy ,Ammie wannan ce kaɗai zai ɗabemin kewar rashin ta kusa dani. Ina Son Umaima ,Ina son ta , but she Go and live me aside. Why she do that to me???. Daddy Bana da kyau ne ,ko kuwa bana da matsayin da wata ɗiya kaman Umaima zata soni ne??. Dad you now what??? Yayi maganan cike da murya ta maye ,kana yace akan ta na fara jin daɗin Sex ,I need her." Kamin ya rufe baki ne yaji mari tassssss". Cikin wani irin huci Daddy Ke kallon Umair kamin yace" Tashi ka fucemun daga falo mara kunyan wofi . Umair kai naka giyar kudin da ƙuruciyar da haka yazo maka?. Miƙewa yayi ya na tangadi. Nigeria is urs'. Bana wa bane ba, since before now na tsani Nigeria , a yau zan ɗauki visa na zan koma ƙasar Momy na nayi rayuwa ta . Yana gama faɗin haka ya juya yana tangadi ya nufi hanyar fita daga falon. Umair .!! Ammie ta ƙwada kirar sa idon ta na zubda Hawaye . Bai bi takan ta ba ya sa kai yana ficewa daga falon. Cikin sauri Ammie ta juya tana bin bayan sa tare da kirar sa.

Kar ki taka ko nan da can.! Taji Muryar Daddy Yayi maganan a fusace . Cak taja ta tsaya tana kallon sa hawaye na bin kumcinta . Daddy ya Zamu yi mu sa Umair farin ciki. Ammie magana kika tsaya yi , Ya Umair fa ya fita ,kuma ba a hayyacin sa ba , nasan ma da kansa zaice zaiyi driving lemme go and escort him . Cewan Surayya da duk abun da ya faru tana daga bayan su tana jin su. Ammie ki daina kuka zan sa yaya Ya fasa tafiyar nan duk yanda zanyi zanyi naga bai koma can ƙasar ba. Don Allah Surayya kiyi kokari wallahi mukayi kuskure Umair ya bar Nigeria to ganin sa sai yayi mana wuya. Ammie na sani . Da gudu Surayya ta bar falon tare da nufar farfajiyar gidan tana ƙawsa kirar Ya Umair.!!!!

*AUNTY AISHA MMN TEDDY*
*Q*

*Littafin THE SEXY BOSS na kuɗi ne ban yarda ki karanta mun ba tare da kin biyani haƙƙi na ba... Regular group ₦300...Vip group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko kuma ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932 Idan VTU transfer zakiyi ki tura kai tsaye ta wannan number 09061466409*

Da wani irin gudu Surayya ke bin bayar Umair wanda tuni ya isa ga moton sa yana kai hannun sa tare da buɗe murfin moton , jin Kirar sunan sa Da Surayya keyi yasa shi dakatawa daga shiga cikin moton yana juyowa tare da bin ta da kallo a miskilance. Isowa Surayya tayi tana haki don gudun da tayi kana tace " Pls Yaya Umair Kar kayi driving da kan ka , idan kayi a wannan halin da kake ciki komai ka iya faruwa da kai . Bari Ni na kai ka. Duk maganan da take bai bata amsa ba har ta dire ayar ta , baya yayi yana Matsawa ita tare da juyawa yana nufar side ɗin mai zaman banza , ita kuma ta shiga daga ciki tana fara driving ɗin moton , tare da barin farfajiyar cikin gidan.! A hankali take tafiya tamkar ƴar koyo domin jikin ta yayi sanyi , Shiru tayi tana tunanin kalaman Yayan nata akan UMAIMA ,wannan wacce irin marar rabo ce da har ya Umair zai ce yana Son ta ,ta zaɓi Aurar talaka akan Yaya na.? Wacece ita? Niko zan so naga ita ɗin wacece??? Mai ta taka Ƙyau ko dukiya..? Abun da Surayya ke faɗi kenan a zuciyar ta tana driving tare da kallon Umair ta gyefen ido. Addu'a Surayya keyi ALLAH yasa Umair yayi barci ,wanda juyowa n da zatayi taga tuni barci yayi gaba dashi. Murmushi tayi tana furta Alhmdllh . Gidan sa na Abuja ta wuce da shi kai tsaye , bin gidan na tsaya yi da kallo , ina mmkin ƙayatuwar shi , wato shi ko a ina sojoji yake sakawa suna masa gadi kenan. ,don anan ɗin ma sojojin ne securities nasa . Horn Surayya tayi nan take aka buɗe mata Gate ɗin tana kutsa moton izuwa cikin farfajiyar gidan . Shiru Tayi tana cikin moton kusan mintuna Biyar tana tunanin ya kuma zata yi da Umair shi da yace " Airport kuma ta kawo sa cikin gidan sa .

Juyawa tayi tana bin securities masu fararen kaya na gidan ,da kowa ke aikin gaban sa. A hankali ta fice daga moton tana nufo side din da Umair yake kana tasa hannun ta a saman nashi tana ɗan girgiza shi da faɗin " Yah Umair .! Yaya Umair.!! Tana ƙara girgiza hannun sa . Buɗe lulun idon sa yayi yana sauke su akan fuskar Surayya da ta sakin masa murmushi kamin tayi magana ya fito da kafarsa waje yana fitowa daga moton . Kama shi tayi tana rungumo shi wai ala dole ga mai iya Bada kula ,hannun ta ta zagoyo dashi ta bayan sa . Murmushi yayi a haka suka isa har falo. Ni ma dai kaina nayi dariya ganin. Surayya ce zata iya rike yayan nata wai gudun kar ya faɗi a maye . Gata can ƙasan kafaɗan sa . Ko da suka shiga daga ciki direct Bedroom ɗin sa ta wuce da shi ,tana ƙwantar dashi a saman lafiyayyen Bed ɗin sa mai shegen ƙyau. Lumshe idanun sa yayi Surayya na rufe sa da Blanket tare da cewa " Ya Umair barci mai daɗi". Bata jira jin mai zai fito daga bakin sa ba ta juya tare da barin Bedroom ɗin tana nufar falo. Bin falon ta tsaya yi da kallo , sai taji wayar ta ta fara ruri . A hankali tasa hannu tana picking call ɗin kana ta kara A kunne tana furta" Hello Ammie". Yana lafiya ko?. Abun da Ammie ta tambaya kenan . Eh Ammie y samu barci ne yanzu haka , zan zauna da Yaya anan Har zuwa lokacin da zai manta da wannan yarinyar a zuciyar sa da rayuwar sa . Kuma zanyi kokarin ganin ya amince ya zauna a nan Nigeria bai bar ƙasar nan ba.

Hummmm Ajiyar zuciya Ammie ta sauke kana tace " Ohk to ba damuwa , Allah ya taimake mu , ka sanyaya zuciyar wannan bawa naka". Amin Ammie cewan Surayya tana ƙare cewa " Sai munyi waya .Ohk Ammie tace tana datse kirar . A hankali Surayya ta nufi under ground don anan ɗakin da duk tazo gidan anan ɗakin ta yake . Nufar Bedroom din ta tayi wanda anan ta tadda komai tsaf kaman tana nan a koda yaushe,don rabon ta da Bedroom ɗin tafi shekara guda . Fitowa tayi kai tsaye ta nufi Kitchen don haɗa mawa Ya Umair dishes sanin kan ta ne ya farka daga barcin sa zai iya buƙatar abun da zaici ,wannan yasata nufar Kitchen ɗin don fara shirya masa Abun da zai taɓa .!

***

Ɓangaren Umaima kuwa bala'i yanzu take don Yayan Ashiru wato Yaya Uwauwa fita tayi daga ɗakin nata wanda yake falle ne ɗaya , babu abun da aka sanya sai gado da durowa , da kujerar mai cin mutum biyu guda ɗaya komai nata na ɗan talaka ne . Fitar da yaya Uwauwa tayi gidan ta bari baki ɗaya ,kowa ta gani a hanya sai ta furta gashi can Umaima daga kawo ta ɗaki ta fara amai ,ta taho masu da cikin shege , wallahi Ashiru ba zai shiga ɗakin ba yanzu iyayen ta sai sun zo sun ɗauke ta . Haka take sambatu na masifa kowa ta gani a layi sai ta fallasa , kamin magana ya iso gidan su Umaima kunsan ƙaramar unguwa tuni magana ya gama karade layin da ko'ina . Koda ta isa gidan su Umaima cikin dandazon dangi da ƴan uwa da abokanan arziki a wannan lokaci ta kama ƙugu tana faɗin su taho su dauki yar su ,dama sun san yar su watsatstsiya ce suka liƙa mawa ƙanin su , to su zo gashi ta kunso ɗan zina , maza su taho su tattara koman su ,su fitar da ita daga gidan su . Kallon ta Kowa keyi yayin da Yaya Hannatu ta nufo Yaya Uwauwa tana cewa " Kaman ya ban gane ba.? Umaima yarinya ƙarama kuma kuka taho mana da wannan sharrin akan ta?. Sharri ai mu bamu saba sharri ba ,gashi can ta kilaya Amai kaman zata fidda yan hanjin ta kuce sharri . Hummmm ko wacce burga zakuyi kuyi dai ,dama kun san yarinyar nan watsatstsiya ce , to mu gidan mu duka ba shegu bane . Hannu yaya Hannatu ta ɗaga tana shirin Wanke fuskar Yaya Uwauwa da mari Nan Umma tayi saurin riƙewa tare da faɗin " A'a dakata Hannatu Rabu da ita maza yanzu kuje ku dawo mun da Umaima .!

Wani irin zafi zuciyar yaya Hannatu keyi kana tace " Wallahi kinci Albarkacin Umma ,da badon haka ba,sai kin yaba ma aya zaki ,meye a dangin naku ban da tsiya da tijara,kuma gashi kunzo kun nuna mana hali ai . Kuma kusani Wallahi Umaima ta bar Ashiru har Abada . Juyawa yaya Hannatu tayi bata jira jin na bakin Uwauwa ba ,ita da su Lawisa kusan su huɗu suka ɗauki mayafi suna nufar gidan su Ashiru don dawowa da Umaima . Yayin da Yaya Uwauwa take wani zambaɗa sauri don tuni tayi gaba ta isa gidan basu zo ba . Da isan ta ne ta shiga ɗakin da har yanzu Ashiru bai fito daga ɗakin matan gidanab fiye da goma sha sun cika dakin kowa na Allah wadai . Itako Umaima sai kuka . Ji tayi Yaya Uwauwa ta fizgota tana yo waje da ita zuwa tsakar gidan. Dai dai su Yaya Hannatu na isowa . Ke baiwar ALLAH iskan cin ki ya fara yawa fa.!

*Zamu kammala book 2 don haka idan mun kammala book 2 masu saye ₦300 ne complete , Idan kuma duka muka kammala masu sayen complete 2 and 3 ₦600 ne .*

*AUNTY MMN TEDDY*
*R*

*Littafin THE SEXY BOSS na kuɗi ne ban yarda ki karanta mun ba tare da kin biyani haƙƙi na ba... Regular group ₦300...Vip group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko kuma ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932 Idan VTU transfer zakiyi ki tura kai tsaye ta wannan number 09061466409*

_Happy New year to u and all ur near dear ones💃 wish you all only the best..great health and happiness, peace, sucess and learning in Al u Do...#Welcome 2023🕊️_

*END OF BOOK 2*

Yaya Hannatu ne yi ɗammara da mayafin ta tana kallon Yaya uwauwa da take daɗa surfa masifa. Ke baiwar Allah na rantse da ALLAH kika kuma taɓa Umaima sai kusa zubar maki da jini ,kawai daga yarinya tayi amai shikenan sai kuce ciki , wato ba'a amai haka kurum kenan. To bari gargaɗeki mu mun karbi Umaima , kuma kisani daga yau mun rabata da ke da ahalinki dashi kan shi Ashirun rabawa ta har Abada .don haka kuja kunnen ɗanko. Idan kuma yayi kuskuren kawo ƙafarsa ko bakin sa to duk Abun da yabiya baya shiyasa Ni . Yaya Hanne tana gama maganan taja hannun Umaima dake kuka kaman ranta zai fita. Yaya Hannatu don ALLAH kuyi haƙuri kuskure ne da rashin fahimta ,amma ina son Umaima ,ficewa yaya Hanne tayi ,kana Lawisa ta tsaya tana kama ƙugu tare da bin gidan da matan Gidan da Kallon uku saura ƙwata . Humm shiyasa aka talaka bai ya samun wuri ba. Ku kalla gidan da Umaima ta fito ba kaman wannan gida da aka jefota Aure ba. Me kike nufi kenan? Cewan Yaya Uwauwa tana matsowa kusa da Lawisa da ta cigaba da cewa " Eh mana ai gaskiya na faɗa . Kalli da Ashirun wani zagalo dashi ,ai wallahi Umaima ta wuce mawa Ajin Wannan da gidan nan baki ɗaya ,dama karamci aka maku amma kun nuna baku san hakan ba.

Kamin taji wani magana da zai fusata ta ta juya tare da barin gidan Su Ashiru da ƴan biki cike da dangi da yan uwa .

***

Da sanyin safiya ne Surayya ta miƙe cikin sauri ganin yanda rana ya fito har 8:35am bata farka ba sai yanzu . Saurin fitowa tayi izuwa falo , wanda dai Umair yana bamawa wani mai aikin gidan nasa , jakarsa irin babban nan na matafiya wanda sojoji ke tafiya dashi. Saurin saukowa Surayya tayi tana hugging din Umair tare da cewa " morning Yah Umair. Shafa kan ta yayi yana

cewa " Kin tashi.? Gyada masa kai tayi alamun eh. Ohk yanzu ki shiga ciki ki kimtsa , ga breafast ɗin ki a dining area , Ni zan wuce Germany yanzu zanbi jirgin 9:00am ,nayi magana da Julayb zai zo ya ɗauke ki ya mayar dake gida. Ƙwallah ne ya ciko idon ta ,kana a shagwaɓe tace " Ya Umair me yasa ba zaka zauna anan ba Pls ya Umair ka zauna damu. Ammie zata nemo maka mata mai kyaun gaske fa fiye da Umaima.!

Ba zaku sami kamar Umaima ba ita ɗin ta daban ce , Zaman can zaifi mun fiye dana zauna anan a kowacce rana tunanin ta nake yi bana iya hasala komai Surry , matso kiji . Yayi maganan yana kallon Surayya da idon ta ke fidda ƙwallah. Baki ji komai ba?.

Kallon sa Surayya tayi cike da rashin fahimta kana tace "Yah Umair banji komai ba. Hummmm nisawa yayi yana sauke ajiyar zuciya kana yace " Har yanxu jiki na ƙamshin turaren ta yake yi . Bazan taɓa iya mantawa da Umaima ba. Je ki shirya . Yana faɗa mata haka ya fara takawa yana barin falon . Bin sa da kallo tayi kawai sai ta fashe da kuka tana fadawa saman kujerar falon , Tabbas da gaske ne ya Umair ya kamu da So.! So zazzafa ,wanda zai iya saka shi ko wani hali . Cikin sauri ta nufi gidan ƙasa don ɗaukar wayar ta ta sanar mawa Ammie don ta dakatar dashi daga wannan tafiyar .

***

Bayan tafiyar Hajiya Mulayka ne Hajiya Turai ta fara faɗawa Duniyar tunani , wanda sam ta gaza fiddo mawa kan ta da mafita . A hankali ta fara tunano mawa kan ta mafita daban daban ,kana Tana wannan kaiwa da dawowa ta furta' Mai jidda". Shiru tayi tana tunani kamin tace " Anya wannan yarinyar nata tana da Raye kuwa?? . Rabona da wannan a halin Kusan shekara goma sha takwas tun da ta haihu ta rasu ,ban kara komawa wannan dangin ba ,dole na fara kira na tambaya , a yanzu ba sharri nake son kulla masa ba ,neman wanda zai tarkata mun kaf dukiyar sa nake yi. Wanda dole babu wacce zata iya sai jini na.! Dole a satin nan na leƙa ƙanwar mahaifiyata wato Hajiya Balki.

Wai shin wacece Hajiya Turai.??? . Hajiya Turai ta kasance macace wayayyar gaskiya , tun tana yammatan cin ta haka take , mahaifin su shine Ƙani Wurin Hajiya Balki , wato kakan Umaima . Su biyu Allah ya basa , daga ita Sai ƙanwar ta wato Umman Umaima da ta rasu Sunan ta bilkisu . Tun tasowar Hajiya Turai ta nuna ta fi ƙarfin a nuna wannan dangin ace yan uwan ta . Idan ka ganta a to mutuwa ne wanda ya zaman mata dole sai tazo ko tarar biki bata zuwa bare kuma ta ɗauki jiki ha ka kurum ta taho. Tun da Umaima take sau ɗaya ta taɓa ganin wanda a yanzu ko ta ganta zata wuce itama ta wuce basu san juna ba. Iyayen Hajiya Turai da Balkisu duka basu yi tsawon rai ba ,don mahaifin su ya rasu ita Hajiya Turai tana da shekara 15 a duniya yayin da Umman Umaima keda shekara sha ɗaya . Ba kuma ayi shekara ba Mahaifiyar su ta rasu . Wannan yasa Hajiya Balki cewa a dawo mata dasu gaban ta da zama. A lokacin da Hajiya Turai ta fara yammatan cin ta ne , ta gummaci da zaman gidan Hajiya Balki gwara taje G.R.A aikatau daganan tasan zata lalubo miji na nuna mawa sa'a kalan wanda take

so da buƙata. Ita dai Balkisu a gaban Hajiya ta zauna yayin da ita Turai ta debe jiki aiki a G.R.A ,wanda ita ko aikin ne ba a kowani gida take yin shi ba ,sai taga irin Commisioner ko irin manyan masu kuɗi .a haka ne ALLAH ya bata ɗaya Tamkar da dubu mutum mai tawakali Son talakawa a kuma wannan lokaci n yana kujerar sa na commioner of finance , a haka abu kamar wasa yakai ta ga Auren Alh Ahmad moddibo a wannan lokacin ,ko iyayen ta bakowa ta nema ba ,don iyayen duniya da kalan dangi su suka daura mata Aure. Tun da tayi Aure bata ƙara bibiyar dangin ta ba , rayuwar ta kawai take kusan shekara talatin. Sau biyu tazo tun bayan Wannan nan Aure nata shine rasuwar mahaifiyar Umaima Balkisu , Wanda auren Balki babu ita ba ƙafarta sai dai mutuwar ta da tazo ,a ranan da tazo a ranan ta juya. Bata ƙara bibiyar su ba ,sai da Umaima takai shekaru Biyar ne ,sannan ta tazo tayi mata abun arziki tun daga nan har iya yau Hajiya Turai bata ƙara zuwa wurin dangin ta ba ,haka koda sun kirata a waya tun tuni bata ɗauka. A yanzu ma babu wanda yasan layin ta. Don ta share kowa a lissafin Rayuwar ta .

Cigaban labari.!
Juyawa tayi tana sakin wani irin murmushi ,kana tace " kece zaki mun komai.

***

Ɓangaren Umaima kuwa , Tasa ta Umma tayi tana hawaye tare da faɗin Umaima waye yayi maki Ciki? Umaima abun kunya kika ɗauko mana.! Kun tasa ta kuna ta mata magana bayan kunsan waye yayi wannan cikin eiye kuka wannan maganan . Auwalu ne ,kuma hukuncin da bulalai ne dole a kai shi ga Shari'a ,ai sace ta yayi. Cewan Hannatu tana haki. Umaima faɗa mana waye yayi Maki.... Baba Sule ne ya shigo Ɗakin da wani irin murtikeken bulala , nan take ya fara zuba mawa Umaima tana ihu tare da faɗin Baffa don Allah kayi haƙuri , wallahi ba Auwalu bane.wani bulala ya zuba mata shaffff a gadon bayan ta ,wanda yasata gantsarewa tana furta " Wayyo Ni Umma na shiga . Waye yayi Mali wannan kunyar? Cewan Baba Sule yana dakatawa tare da yin numfarfashi. Ba Auwalu bane.! Tayi maganan ciki. Dassher murya wacce da kyar ya fita. Waye??? Cewa Baba Sule.
"UMAIR ".

Ba su Umma ne kaɗai suka firgita ba har Bana sule sakin bulalan yayi nan take yana furta" Umair.! Babu shakka shine wallahi fyaɗe .! Kawai sai ta kuma rushewa da kuka mai ban tausayi da tsuma zuciya .

Girgiza kai Baba Sule yake na mamaki , kana yace ' Hannatu bata ruwa
Umma taho ina Son magana dake .a hankali Umma jiki a sanyaye ta fita tana bin bayan Baba Sule .

***

Kaman yanda Umair ya ƙudrta haka ya faru safiyar littinin ya yi masa ne ƙasar Germany ,

wanda tun da ya isa bai iya hasala mawa kan sa komai ba.layin sa ya sauke ƙasa yana maida na wannan kasar don bai bukatar kira daga kowa , Julyb ya tuna da shine ya fara sanar masa da An ɗaura masa Umaima aure da Wani ba shi ba. Cije lips ɗin sa yayi na kasa tana furta me yasa bani ba?. Na bar Nigeria bari na har Abada.!

***

Hajiya Turai ban gane me kike nufi ba? Kina nufin yanzu Bakya bukata ta a aikin da zanyi maku na Umair? Cewan Ru'aifa tana fiddo da idanun ta ga Hajiya Turai ,wacce take kishingiɗen cikin doguwar rigar lace da akayi masa ɗin kin bubu. Sosai ya fito da kuɗin da kuma hutun ta. Ƙwarai ki zame hannun ki , buɗe jakarta tayi tana fiddo mata da raba dubu ɗari guda biyu 200k tana wurga mata kaman takardu kana tace 'Na samu wacce zata aure shi , kuma nasan mahaifin sa dole zai Amince da hakan tun da yar ƙanwata ce marigayi ya . Hannu Ru'aifa tasa tana ɗaukar kudin kana tace " Wannan ladan wahalar da nayi maki ne kika biyani . Amma ki sani ina SO.! tayi maganan tana kecewa da dariya ta yan bariki kana tace " Baki fahimta ba ko Hajiya?. Umair nake so , kuma ki rubuta ki aje bazan taɓa yarda Umair ya kuɓce mun ba har ya Auri wacce kk mafarkin ganin ya Aura. Sai anjima.! Miƙewa Ru'aifa tayi tana barin hajiya Turai anan wurin . Kamin daga bisani Hajiya Turai ta sheƙe da dariya tare da faɗin Yaro yaro ne.!

***

Ɓangaren Ammie kuwa hankulan ta ya tashi a ranan da Umair ya bar Nigeria kwana tayi bata rintsa ba tana kai Addu'oin ta ga mahalicci , haka yau gashi kusan kwanan sa uku amma ko takira baya shiga .shi kan shi Daddy Hankalin sa ya tashi ,daurewa kawai yake irin nasu ta manya .don a idon Umair kawai ka kalla kasan ya kamu da mahaukacin so.! Wannan yasa Shi kan shi yake masa addu'a da ma duk wani Abu da yake yi marar kyau.

***

Daddy ne yayi shiru yana sauraren maganan Hjy Turai , kamin ta cigaba da cewa " Yar ƙanwata ce Uwa ɗaya Uba daya , Balki kike magana?. Cewan daddy Yana Kallon Hajiya Turai eh kwarai ita. Ohk yanzu Umair baya a natsuwar sa ,idan muka ce aure zamu sa shi a tension da yawa . Mu basa nan da 3 to 6 mount mu gani. Ni da kaina sai nayi tattaki na nemo masa Auren Yarinyar...!

*Na so ace mun kai Z sannan zamuyu completing book 2 ,ammma anan na kawo ƙarshen littafin THE SEXXY BOSS na biyu ,sai mun haɗu a book 3 . Masu jirar COMPLETE book 2 ₦300 ne kacal. Zaku iya Turo da katin MTN ta wannan number 08081202932 ko ki tura ta wannan account 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank*

*ANTY AISHA MMN TEDDY*